



Kare da mage sun yi shiri.


Za su yi tsere.



Ranar tsere ta zo.


Kare ya shirya.

Mage ma ta shirya.




Ruwan sama ya zo.


Mage ta fasa tseren.



Kare ya ce mage na tsoro.

Mage ta ce ba ta tsoro.






Ruwan sama ya tsaya.

Kare ya shirya.

Mage ma ta shirya.





Sai ɓera ya wuce da gudu.

Mage ta bi ɓera da gudu.



Mage ta bi ɓera da gudu.

Kare ya bi mage da gudu.

Bera ya shiga rami.

Mage ta gaji.

Kare ya gaji.